# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tuntuɓar juna tsakanin addinai: Haɗin kan mutanen Sodangi
## Kashi na goma: Ranar sabunta zumunta

Wanda ya rubuta: Romie Singh
Wanda ya tace: Katrin Ogunsade, Naïma Guira
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Tafida: | ɗan shekara 17 |
| Baban Tafida: | ɗan shekara 50 |
| Dauda: | ɗan shekara 17 |
| Layla: | 'yar shekara 16 |
| Saima: | 'yar shekara 16 |
| Ɗanjuma: | ɗan shekara 16 |
| Malam Isma'ila: | ɗan shekara 43, baban Layla |
| Fada Bana: | ɗan shekara 49, kawun Dauda |
| Maigida Ranau: | ɗan shekara 49, baban Dauda |
| Nas Rakiya: | 'yar shekara 28 |
| Hassan: | ɗan shekara 12, ɗan'uwan Layla |
| Alƙalin gasa | |

**MAI GABATARWA:**
Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin kashi na goma kuma na ƙarshe a jerin wasan kwaikwayonmu na shirin "Ji Ka Karu" mai taken "Haɗin kan Mutanen Sodangi", wanda aka shirya a kan yadda addini da siyasa suka haddasa zaman doya da man ja tsakanin wasu al'ummomi guda biyu, da gidaje biyu. A wannan kashin na yau mai suna "Ranar sabunta zumunta" za mu ji yadda Dauda da Layla suka bayyana wa iyayensu irin abin da suke shiryawa a tsakaninsu nan gaba. Da farko dai, sai mu saurari yadda baban Tafida yake bayyana wa ɗansa wani sirrinsa da yake ɓoye da shi shekara da shekaru.

**Fitowa ta 1: A gidan su Tafida**
Baban Tafida, Tafida

**BABAN TAFIDA:** Kana ji ko Tafida, wannan al'amari fa ya faru ne tun kafin zuwanka duniya, wato a lokacin ba a haife ka ba.

**TAFIDA:** To. Baba, me ya faru?

**BABAN TAFIDA:** Wannan matar da ka gani a cikin hoton nan da ke kan teburina, odita ce, wato mai binciken kuɗi. Akwai lokacin da aka fuskanci wasu 'yan matsaloli a cikin ofishinmu, sai aka turo ta don ta bi diddigin harkokin kuɗin da aka yi. Abin dai ya ɗauke ta 'yan kwanaki. Takan yi aiki har zuwa cikin dare. To, ta haka dai har muka san juna.

**TAFIDA:** Haka ne. Wato dai sai ta zamo budurwarka, kuma daga baya sai kuka ɓata ko? Shi ne dai zancen ko?

**BABAN TAFIDA:** E to, ba haka ba ne. Gaskiya a lokacin muna matuƙar soyayya da juna. Duk da cewa ita Musulma ce, ni kuma na

fito daga gidan da addini ma bai dame su ba sam-sam. Hakan sai ya sa muka fuskanci matsaloli.

**TAFIDA:** To, ina jinka. Wace ce ita? Ko kuma ba za ka iya gaya min ba?

**BABAN TAFIDA:** Sunanta…sunanta Nafisa.

**TAFIDA:** Nafisa?

**BABAN TAFIDA:** Za ka san ta. Ita ce matar Malam Isma'ila kafin ta rasu.

**TAFIDA:** A'a! Matar Malam Isma'ila? Wai! Kai Baba? Me kake so ka gaya mini ne? Ba dai babar Layla ba. Kai! Wai! To, shi jinjirin da ke cikin hoton kuma fa, wane ne shi? Kar dai ka ce min shi ne...

**MAI BA DA LABARI:**
To, daga ƙarshe dai kome ya fito fili. Ashe dai ba a banza Tafida yake ji yana ƙaunar Layla ba, ashe ita 'yar'uwarsa ce! Babarta ta auri Malam Isma'ila ne a lokacin tana da yaron ciki, shi kuma Allah bai sa ya lura ba. Daga baya sai ta haifa wa Malam Isma'ila ɗa namiji wato Hassan, kuma ba ta taɓa faɗa masa gaskiyar al'amari dangane da Layla ba, har ta mutu. Wannan ke nan. A yanzu haka ga 'yan Kwalejin Zumunta da su da mutanen garin Sodangi can suna bikin Ranar Sabunta Zumunta!

**Fitowa ta 2: A Cibiyar Sabunta Zumunta**
Dauda, Ɗanjuma, Tafida, Alƙalin gasa, Saima, Layla, Malam Isma'ila, Nas Rakiya, Hassan, Maigida Ranau, Fada Bana

**ƊANJUMA:** Taso mana Tafida! Yaya za ka zauna haka kai kaɗai? Mu ne fa muka yi nasara a Gasar Muhawarar da aka yi, ai kuwa ya kamata a ce shagalin nan da kai ake yi!

**DAUDA:** Gaskiyar Ɗanjuma fa. Don Allah Tafida ɗauko kyamararka mu ɗauki hoto, mu manyan yaran Kwalejin Zumunta. Kun shirya? Ɗaya, biyu, uku,… yeeeeh! … Gaskiya abin ya yi! Zo mana Tafida, muna so ka ɗaukar mana hoton Saima da Layla, yayin da suke kai wa ga nasara a gudun mita 400 da suke yi!

**TAFIDA:** Kai Dauda tsaya! Ka san fa wasu mata Musulmin ba sa so a ɗauke su a hoto. Yana da kyau mu tambaye su tukuna.

**DAUDA:** Kai, ba wani abu. Ai sai da Madam Titi ta tambayi kowannensu cewa za a sa hotonsu a cikin mujallar makaranta da kuma jaridar su babanka.

**TAFIDA:** To shi ke nan. Kai! Amma fa ni rigar nan mai dogon hannu da wando da kuma hijabin da 'yan matan Musulmi suke sa wa suna matuƙar burge ni. Bari in ɗan matsa kusa-kusa.

**DAUDA:** La Ɗanjuma, ka ga su ma mazan sun sa riga mai rufe musu jiki. Na ji ana cewa wai rigar ta musammance, ba ta da nauyi sam. Shi ya sa ma ka ga ba sa gumi.

**DANJUMA:** Gaskiya dai yanzu an sami ci gaba. Kun ga kowa yanzu yana da damar shiga cikin harkar wasanni ke nan.

**ALKALIN GASA:** Kun shirya? … Mu je zuwa…

**HASSAN:** Yauwa! Kara gaba! To mana, Layla!

**MAL. ISMA'ILA:** To mana. Yauwa 'yata ta kaina. Har yanzu dai ita ce ta uku! La! Hassan, ka ga Nas Rakiya ɗinka ta asibiti!

**RAKIYA:** Au, Hassan, Malam Isma'ila! Ina wuninku? Yauwa, ta shiga gaba! Kara gudu! Yauwa!

**HASSAN:** Yauwa! Layla ce ta ɗaya, Saima ce ta biyu! Yeeeh!

**GABA ƊAYA:** A gaishe ku 'yammata! Yeeeeh!

**SAIMA:** A gaishe ki, Layla! *Congratulations!* Kin taimaka mana mun ciwo kofi! Tafida, ko za ka ɗauke mu hoto!

**TAFIDA:** Ba dole ba! To, ku yi ɗan murmushi mana! … Madalla!

**LAYLA:** Mun gode, Tafida! La! Bari in gani. Kai! Ai kuwa hoton ya yi kyau!

**TAFIDA:** Zan wanko miki naki. Wannan ai abin tarihi ne.

**LAYLA:** Na gode, Tafida! Ko kana so ka ba ni shi ne a matsayin kyautarka ta ban kwana?

**TAFIDA:** Wannan ai ba…wannan ai wani…kin ga, ni ina so ne na...

**LAYLA:** La! Dauda kalli, ga babanka can da shi da kawunka suna magana da babana. Zo mu je wurinsu. Tafida sai an jima!

**MAI BA DA LABARI:**

Sam Tafida ba zai taɓa gaya wa Layla abin da ya ji game da ita ba, wato game da dangantakarta da mahaifinsa da babarta, da kuma yadda tsakaninsu yake. Shi dai Tafida kawai so yake ya ɗan gan ta na minti ɗaya a matsayin

’yar’uwarsa. Amma ita hankalinta duk ya koma kan yadda ta ga zuriyar Umaru da ta Dembele sun tsaya suna magana da juna.

**DAUDA:** Kai! Yau ga abin mamaki! Ga Malam Isma’ila, da Baba, da Fada Kawu!

**FADA BANA:** Yaya dai Dauda. Fada wa?

**DAUDA:** Yi haƙuri, Kawu! Ai wannan laƙabin da na sa maka ne!

**MAL. ISMA’ILA:** A gaishe ki Layla, ’yata ta kaina!

**HASSAN:** A gaishe ki babbar yaya. La! Kin ga Nas Rakiya can, da ita da ’yarta Rifkatu. Idan muka kai cika shekara goma sha shida, za a sa mu a Kwalejin Zumunta ni da ita! Baba ya ce ba abin da ba zan iya ba!

**LAYLA:** Lalle wannan labari ne mai daɗi! Kuma to, ka san su Yahudawa ne fa.

**HASSAN:** ’Yan ƙabilar *Lemba* ne su. Ai ni da ita mun sha musayar ra’ayi a kan abin da Littafin Yahudawa, wato Attaura, da kuma namu Littafin, wato Alkur’ani, suke koyarwa. Ni so nake ma idan na girma na yi nazarin tarihin addinai dabam-dabam!

**LAYLA:** Zo mana ɗan ƙanina! Ai ka san ina ji da kai!

**HASSAN:** Saboda me? Ai ba ni na yi nasara a tseren mita 400 ba, ke ce!

**LAYLA:** Kai ma ai ka sha naka tseren Hassan, tun da ka tsallake tarnaƙin da ya raba mu da abokan arziƙi da kuma

maƙwabtanmu! Na tabbata Kwalejin Zumunta za ta yi alfahari da kai!

**DAUDA:** Baba! Ina so ni da Layla mu…

**LAYLA:** Baba Ranau, Baba! Dauda yana so ya dinga zuwa wajena.

**MAI GIDA RANAU:** Lalle! Wai yau ga yarinya na sanar da ni cewa ɗana zai fara zuwa wajenta zance! Haƙiƙa zamani ya sauya! Mu kuwa kin ga a tamu al'adar, dole sai mun kawo shanu gidanku tukuna, saboda a albarkaci wannan soyayya taku.

**LAYLA:** Lalle abin na yi ne!

**MAL. ISMAI'LA:** Na gane abin da Maigida Ranau yake nufi, kuma ni ma na amince da haka. Mu ma muna da wata al'adar da muke yi da ta yi kama da wannan a tsakanin al'ummarmu. Amma dai, mu ci gaba da tattaunawa don mu fahimci al'adun juna. Dauda, ya kamata ka san cewa ni ba zan tilasta maka bin addininmu da al'adunmu ba. Na san kai da Layla za ku tafi jami'a wadda take nesa da gida. Ya kamata ka san cewa tana da manema da yawa, don haka, ka riƙe ta amana. Don haka ku kula da junanku.

**FADA BANA:** Ina ganin za mu iya ci gaba da riƙe al'adunmu har ma kuma mu karɓi na wasu. A lokacin da Rabaran Haruna Emah na Cocin Karismatic ya gudu da kuɗin 'yan cocinsa sai na fahimci cewa, yawanci siyasa ce take ratsowa cikin al'amuranmu, ta haka muke fake da bambancin addini don biyan buƙatunmu. Wannan gaskiya bai dace ba. Malam Isma'ila a matsayinka na ɗan Majalisar Raya Kasa, sai na ga ra'ayinmu ya fi zuwa ɗaya da kai, fiye da waɗanda muke addini ɗaya da su.

**MAIGIDA RANAU:** Ba shakka ɗan'uwana! Dukkanmu muna son ci gaba da yalwar arzikin al'ummarmu! Wannan ita ce fa Zumunta, kuma ita ce take haɗa kawunanmu a kowane lokaci.

**MAL. ISMA'ILA:** Tabbas! Kuma a saboda wannan labari na abin arziki da ya same mu, ina so na gayyace ku duka zuwa gidana don mu taya juna farin ciki! Ke ma Nas Rakiya da ke da 'yarki ina gayyatarku. Kuma ina alfahari da Allah ya haɗa ni da ke! Kin ceci rayuwar ɗana a lokacin da ya yi mummunar ƙonewa!

**RAKIYA:** Na gode, Malam Isma'ila. Ai Hassan ne ya buƙaci a cece shi! Ka san ba mu muka halicci kanmu a matsayin 'yan Afirka, ko Yahudawa ko kuma Musulmi ba. Dukkaninmu mun sami kanmu a duniyar nan ne, kuma ba wanda zai rayu ba tare da taimakon ɗan'uwansa ba.

**MAI BA DA LABARI:**

Yanzu dai an zo ƙarshen zangon karatu a Kwalejin Zumunta. Kuma waɗannan abokanai sun shafe shekaru biyu suna tare, kuma musamman ma a shekara ta ƙarshe inda suka fahimci matsayinsu baki ɗaya, kuma Tafida ya fahimci matsayinsa da kuma yadda rayuwa ba tare da hassada da ƙiyayya ba kan taimaka wa lafiyar dukkansu da kuma tunaninsu. Shi ma kuma Hassan ya koyi darussa da dama. Dole ne yanzu shi da waɗannan matasan da ke Makarantar Islamiyya, su haɗu su taimaka wajen gina sabuwar matattarar ɗalibai dabam-dabam a matsayin horo a kan sa wa coci wuta da ya yi. Kuma yanzu su ma suna jin daɗin zuwa wannan makaranta, kuma suna shiga wasannin da ake yi a matsayin ƙungiya ɗaya.

**DAUDA:** Tafida! Tafida, don Allah sake ɗaukarmu a nan kafin mu tafi!

**LAYLA:** Haba Tafida. Tuna baya ai shi ne roƙo!

**TAFIDA:** Haka ne! To, a ina kuke so a ɗauke ku?

**LAYLA:** A kan gadar Sodangi!

**TAFIDA:** A kan gadar Sodangi? Ke da Dauda ɗin?

**DAUDA:** Kwarai kuwa, Tafida.

**LAYLA**: A kan gadar Sodangi kuwa!

**DAUDA:** Mun daina ɓuya daga yau a karƙashin gadar!

**MAI GABATARWA:**

To, masu sauraronmu, a nan kuma muka kawo ƙarshen shirin namu na yau wanda kuma shi ne na ƙarshe a jerin wasannin kwaikwayo da muka kawo muku a kan "Haɗin kan mutanen Sodangi" wanda Romie Singh ya rubuta. Yanzu dai haka soyayyar da ke tsakanin Dauda da Layla ta shafe rikicin da aka shafe tsawon lokaci ana fama da shi a tsakanin iyayensu. Sun gano cewa tattaunawa da haɗin kai da haƙuri da juna da kuma girmamawa addinan juna, su ne hanyoyin dawo da zaman lafiya a garin Sodangi. Kada ku manta, za ku iya sauraron wannan shirin da ma dukkan shirye-shiryen da muka gabatar muku ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe, domin sake jin shirin ko kuma aiko da tsokaci.

**’Yan wasa:**

Abdallah Sani Shu’aibu

Hadiza Jinta

Sadiq Murtala Mansur

Abdullahi Garba

Rabi Salman

Awal Yahya Abdu

Mustapha Nasidi

Yusuf Lawal Gwazaye

Fatima Abdallah

Yusuf Idris

Aisha Mohammed

Umma Suleiman

Tawagar ‘yan Makaranta